**Competitive Scramble is an Evil Ingenuity: Proceedings from the International Conference on the Biography and Songs of Alhaji Abubakar Kassu Zurmi in Heroic Poetry**
A Publication of the Department of Nigerian Languages, Sokoto State University, Sokoto



| ISBN 978-978-62480-5-9 (Print) | ISBN 978-978-62480-5-9 (Online)
DOI: https://doi.org/10.65760/kassu.i1.41 Website: www.ssu.edu.ng |Issue 1 | April 2025|

# Habaici a Cikin Wasu Waƙoƙin Kassu Zurmi

**Aishatu Yahaya Tambuwal**
Sashen Hausa, KwalejinIlimi Ta Shehu Shagari, Sakkwato.

Corresponding Author: **Aishatu Yahaya Tambuwal**
aishayahayatbw@gmail.com
LambarWaya: 08035667111

**Tsakure**

*Waƙawani ɓangare ne na adabin Hausa wadda kuma hanya ce da akan yi amfani da ita wajen gina tunanin al'umma da fahimtar da su wasu hanyoyin gudanar da rayuwarsu. Dabarun isar da saƙonni ta hanyar amfani da waƙa suna da matuƙar yawan gaske. Wannan shi ya samawa ƙasukanyi amfani da hanyoyi iri daban-daban domin isar da saƙonninsu. Wannan maƙalar za ta kalli waƙoƙin makaɗin nan mai suna Kassu Zurmi, da irin yadda yakan yi amfani da habaici wajen gabatar da waƙoƙinsa. Kyakkyawan nazari da sauraron waƙoƙinsa su ne hanyoyin da aka bi wajen gudanar da wannan maƙalar. Sannan kuma an yi amfani da ra'i wanda yake nuni da yadda akan yi amfani da adabi ko al'ada ko harshe a matsayin madubi ko kyallaro al'adun al'umma kamar yadda Ado (2017:87) ya bayyana wajen gudanar da maƙalar. A ƙarshen wannan maƙalar, za a fahimci cewa mawaƙi Kassu Zurmi ya ƙware matuƙa wajen amfani da habaici a cikin waƙoƙinsa wanda wani ɓangare ne na adabin Hausa.*

**Copyright:** *Provided that the author(s) and the source are credited, noncommercial use of the article is allowed, including printing and distribution.*

## 1.0 Gabatarwa

Fasaha baiwace wadda mutum yakan keɓanta da ita. Idan Allah mai rahama mai jinkai, ya yanka wa mutum wani nasibi na fasahar harshe zai zama mai azanci, mai basira, mai sarrafa maganganu cikin hikima tare da karfafa zance. Irin wannan mutum ne yakan zama wanda ya iya harshensa, ya dinga yi yana jujjuya shi, yana sassaka batutuwa. Kuma irin wannan mutum ne yakan zama makaɗi ko mawaƙi ko wani fasihi.

Wannan maƙala za ta yi magana ne a kan tarihin makaɗa Alhaji Abubakar Kassu Zurmi, da nau'oin waƙoƙin Kassu Zurmi da wasu waƙoƙinsa da suka danganci habaici.A cikin wannan maƙala an yi amfani da waƙoƙin Kassu kamar waƙar Labbo Na Amadu, wadda aka yi a shekarar 1970, da waƙar Gondau wadda aka ɗauka a shekarar 1970. Har wa yau an ɗauko waƙar Mamman Ɗangeshe a shekarar 1980. Maƙalata kammala da kawo sharhin habaici daga cikin wasu waƙoƙinsa.

### 1.1 Waƙar Baka A Cikin Adabi

Masana da manazarta waƙoƙin Hausa da kuma su kansu masu ƙirƙiro waƙoƙin,sun bayyana abin da ake nufi da waƙa, ko da ta fahimtarsu ko kuma ta yadda Bahaushe ya fahimce ta.

A ra'ayin Dangambo (2007) ya bayyana cewa:

"Waƙa wani saƙo ne da aka gina shi kan tsararriyar ƙa'ida ta baiti, ɗango,rerawa kari (bahari), amsa-amo (kafiya), da sauran ƙa'idojin da suka shafi daidaita kalmomi, zaɓensu da amfani da su cikin sigogin da ba lalle ne haka suka a maganar baka ba."

A wani wuri kuma ya bayyana ta da cewa waƙa wani furuci ne wato lafazi ko saƙo cikin azanci da aka aiwatarwa ta hanyar rerawa da daidaita kalmomin cikin wani tsari ko ƙa'ida da kuma yin amfani da dabaru ko salon armashi."

Shi kuma Gusau (2003:xiii):Waƙar baka, wani zance na shiryayye cikin hikima da azanci da yake zuwa gaɓa-gaɓa bisa ƙa'idojin tsari da daidaitawa a rare cikin sautin murya da amsa-amon kari da kiɗa da amshi."

Shi kuwa Umar (1980:13) cewa ya yi waƙar baka a Hausa, kamar a sauran harsuna tana zuwa ne a rere cikin sautin murya ko rauji, bata zuma a shimfiɗa gaba ɗayanya sai dai ta zo gunduwa-gunduwa tare da amshi a tsakaninsu."

Waka tsararriyar magana hikima ce da ta ƙunshi saƙo cikin zaɓaɓɓun kalmomin da aka nuna domin maganar ta reru ba faɗuwa kurumba. Wannan yana nufin cewa magana ce da aka zayyana, ba wadda aka aka kara zube ba. Magana ce wadda aka aza bisa sanannun, ko ayyanannun ƙa'idoji waɗanda ke daidaita furuci da sauti, su kuma tilasta zaɓar kalmomi domin dacewarma'ana da furuci. Tahaka ne magana take zuwa babu karo da juna na furuci ko kalmomi, saɓanin magana ta al'ada ko yau-da-kullum. Yahya (1997:4)

### 1.2 Taƙaitaccen Tarihin Kassu Zurmi

Alhaji Kassu Zurmi wanda sunansa na yanka Abubakar, an haifeshi a wani gari da aka kira Magarya ta ƙasar Zurmi, kuma ƙaramar hakumar Zurmi, ajihar Zamfara ta yanzu. Nisan wannan gari kimanin kilomita 24 ne daga Zurmi. Kassu Zurmi ya zauna ne a Kadawa farin da nisansa kamar kilomita 2 kafin ƙarasawa zuwa Magarya wato mahaifarsa, shi kuwa wannan gari wanda aka ce ma Kwatakamar Sabon Garine. Sunan mahaifin Kassu Zurmi, Muhammadu mahaifiyarsa kuwa Maimuna.

Mahaifin Kassu Zurmi Muhammadu Ganga kiɗan farauta ya yi saboda haka ya yi gado ne ba da rana tsaka ya faraba. Ko da yake bai yi ilimin zamani ba, amma Kassu ya ɗan taɓa na Alƙur'ani. Tun kuwa lokacin da ya isa misalin mutum na ya fara bin tsohonsa wurin kiɗan farauta.

Allah maɗaukaki ya yiwa Kassu Zurmi baiwata 'ya'ya masu yawa. A cikin manyan kuwa akwai waɗanda suke tafiya tare da shi wurin kiɗa. A cikinsu akwai Umaru wanda a da ya yi kiɗan tauri wannan ya nuna a yanzu Kassu Zurmi ba ya da wanda ya gaje sa a fannin waƙa.

Hausawa na cewa, "kowa da kiwon da ya karɓe shi, wai makwabcin mai akuya ya sayi kura" To, ɗaya daga cikin 'ya'yan Kassu Zurmi, Aliyu Na'acci sai ya zaɓi bin hanyar

karatun Alƙur'ani.Lokacin da na ziyarci gidansu na iske zauren cike da alluna na almajiransa.

Kassu Zurmi, ya gaji mahaifinsa Muhammadu a wajen kiɗan farauta. Abun da yake kaɗawa kuwa kalangu ne. Amma abin lura a nan shi ne Kassu Zurmi ya taɓa kiɗan noma. To, amma da yake ya yi ne kawai don sha'awa, bai mai da hankali a kan wannan kiɗa ba. An ce dai,'gado girmen ɗa, da yake kiɗan farauta, Kassu Zurmi ya gada sai ya mai da hankali a kansa.Wanda kuwa za a ga kiɗan farauta da kiɗan tauri ne suka fito da shi fili harjama'a suka san shi sosaida sosai. Saboda haka a yanzu idan ba wanda ya san shi ba tunasali, babu wanda zai taɓa tunanin waiKassu Zurmi ya yi kiɗan noma. Da alama wannan ne ya sanya ba a iya samun waƙarsa ta noma ba.

Duk wanda ya san Kassu Zurmi ya san shi na matsayin makaɗin maza.To, kafin a ci gaba, kamata ya yi a fahimci abin da ake nufi da makaɗin maza. Bayan kuwa mazan ne yake yi wa kiɗan jarumai ne waɗanda ko a cikin mazajen lalle sun yi zarra.Don haka, sai jarumi zai iya bari a yanka shi ko a sare shi, sai jarumi zai iya shiga cikin ruƙuƙin daji domin farauta. Haka nan kuma sai jarumine zai iya bin dare ya tafi har wani gari domin ya yiwo sata. To, wanda kuwa yake yi wa waɗannan gwarzaye kiɗa ya cancanci a kira shi makaɗin maza.

A matsayinsa na makaɗin farauta ba wai gidajensu kawai yake bi idan suna ko biki ya kama ba, tare da shi aka zuwa dajin farauta.

## 1.3 Nau'oin Waƙoƙin Kassu Zurmi

Za a rarraba nau'oin waƙoƙin makaɗa Kassu Zurmi zuwa gidaje kamar haka:

- Waƙoƙin Kassu na 'YanTauri' na farko
- Waƙoƙin 'YanTauri na Baya-baya
- Waƙoƙin Kassu na 'YanFarauta
- Waƙoƙin Kassu na |arayi

## 1.4 Ma'anar habaici

Habaici anfi sa shi a cikin maganganun a zanci ta fuska daban-daban wasu na gani dabarace ta danƙulaliyar magana mai yawa a cikin zance ko 'yan kalmomi kaɗan cikin hikima.

**Kamusun Hausa ( 2006):** Habaici na nufin saƙon mutun a taƙaice ta hanyar magana.

Haka kuma habaici shi ne, zance da akeyi da ɓoyayar ma'ana ana gabatar da shi ne da wata manufa ta daban wadda ba kowa yasaniba sai dai wanda akayi habaicin dominsa/ ta yasan da shi ake akan gina habaici ne bisa wani abu da ake tsamanin ya taba faruwa ga wani ko kuma al-ummar baki ɗaya. Musaman halayar marar kyau ko wani abin kunya anayin habaici ne donin a gyara ko kuma ayi nuni ko kuma ɓatanci kai tsaye ga wanda keda waɗannan halayen. Akan jefa habaici ne kai tsaye a gaban mutun ko kuma in ansan yana saurare wato a kai-kaice yasa akama laƙabi da shaguɓe ko kuma gugar zana. Gada da Hadiza (2020).

## 1.5 Habaici A Cikin Waƙoƙin Kassu Zurmi

Shine yi da mutum ta magana a ɓaye. Akan faɗiwasu kamanni ko kuma hali na mutum yadda daga ji za a fahimci ko da wa ake yi. A habaici akwai 'yar gaskiya amma ƙarya takan fi yawa.

Habaici a cikin waƙar Kassu Zurmi gawani ɓarawo da baya fita daji yayi sata sai dai bin ɗakunan mata:

Jagora *: Karamin ɗan duniya ka son rai nai,*
*: manman ya hwaɗa ma ƙoran mata*
*: sai ƙoƙarin ɓantala tasoshi*

*:shegen ɓarayi an nan kanga ma ba ka zanen suna.*
(Waƙar Muhammadu Ɗan Saleh)

A nan kuwaKassu Zurmi yana yin habaici ne ga wani ɓarawo wanda shi ba ya fita daji ya yiwo sata. Sai dai bin ɗakunan mata.

Habaici a cikin waƙar Kassu Zurmi ga wani ɗan tauri:

Jagora : *Rawaya ba ta ratsuwa ai suna,*
*: maidamma bai sake ba,*
*: Rabi'u ɗa nai ka ka yadda,*
*: Doki ukku kay yi min ɗan musa,*
*: Taƙe-taƙe kowane sau nai bai ɓace ba,*
*: Doki ukku kay yi min ɗan musa,*
*: nomau Taƙe-taƙe kowane sau nai bai ɓace ba.*
( waƙar Rabi'u Ɗan Manyan Matsiyata)

An nan habaici ne Kassu ke yiwa abukan taurin Rabi'u Ɗan manyan matsiyata. A cikin baitin sa na farko yana faɗin rawaya bata ratsuwa ai suna. Rawaya gari ne banisa da garin Gusau, yana nufin garin bai shigowa ga abokin taurin shi balle yayi suna ya ce, Maidamma kar ya sake ya yadda. Yace doki ukku yayi mai ɗan musa taƙe-taƙe ko wane sau nai bai ɓace ba, watau a kan girman dawakan duk sahunsu da sunka yi tafiya bai ɓace ba.

Habaici a cikin waƙar Kassu ga mutanen da sunka kashe Sardauna, da wani ɗan tauri Bala ƙara magani:

*Jagora : dutsi sittin da arba'in ɗaya babu,*
*: jama'a ku lissafa,*
*: su adda zuri'a mujadaddi,*
*: da su suka jifar munafuki,*
*: shi ko bawa ya barkace,*
*Ko ya yi dabara ta barkace ɗan nema*
*: Balah adda magani,*
*: Balah ƙara magani,*
*: akwai ka da yaƙi da 'yan uba.*
( waƙar ɗan tauri Balah Konanne Gummi)

Wanan waƙa ta Kassu tana ɗaukar habaici biyu. Na farko yana habaici ga waɗanda sunka kashe Sardauna, yana nufi da tazbaha zuri'a mujadaddi zasu jefe munafukai haka kuma yana habaici ga abukan wasa Balah ɗan tauri da yaƙara magani ma'ana ya ƙara shiri da shina da faɗa da 'yan uba.

Habaici a cikin waƙar Kassu ga Kwazo sabattace:

Jagora : *Da buzu mai gida hili ,*
*: Da su bawa kili da labbo kwanigga ,*
*: Da goge doki ba kaza ba na gaba,*
*: Da iron na yakule da su jibir na ,*
*: Gidan duka su jibo ɗiyan kwali kwandi,*
*: Ba tamnak ku akai ba,*
*: Mutum ya guma ku ya Kalle haƙora nai.*
*( waƙar* Kwazo Sabattace)

An nan Kassu yana yiwa masu ja da su habaici da waɗannan mutane da ya lissafo sama idan suka far musu za su gane kurensu. Shi yassa Kassu yacce musu in sunka gumasu haurunsu na Kallewa.
Habaici a cikine Kassu ke yi wa abukan wasaGidan Duwa:

Jagora : *Babu ruwan Kassu,*
*: Goro ba dangin gero ba ne,*
*: Saboda bauri sauka lafiya,*
*: A adana bauri a kaima mata wasa tayi kyau.*
( waƙar Na Gidan Duwa)

Habaici ne Kassu ke yiwa 'yan tauri yana fadin goro ba dangin gero ba ne, ma'ana ya fi ƙarfinsu. Saboda bauri sauka lafiya.

Kassu Zurmi yana yi wa abokan hamayyar iyayen gidansa habaici dangane da gazawarsu a fagen daga.

Habaici a cikin WaƙarKassu Zurmi dangane da gazawarsu a fagen daga.
A cikin waƙarsa ta jabanda

Jagora *:Ina 'yan KauradDawa?*
*: Nan wani ya shekara bai yi ko kuyya ba.*
*: Amma yay ma mata reno.*
*: Amma yay ma mata reno*
*: Danginsu sun mai kara son ɗan riko mai turbe*
*(waƙar Jabanda)*

Wato Kassu Zurmi yana yin habaici ne ga wani wanda aka sara a wurin farauta har ya kasa noma a wannan damina. Sai dai ya riƙa yi wa mata renon 'ya'ya suna taimakonsa da abin da zai ci ko da yake ba a faɗi ko wane ne wannan mutum ba. Amma mutane wajen da yake nan za su fahimci ko da wa ake.

Dalilin haka ne ma Kassu ya kira shi "Karamin ɗan duniya". Haka shi ma wannan za a iya gane ko da wa yake. Wani lokaci kuwa har iyayen gidan nasa Kassu yake yi wa habaici, saboda wasu dalilai. Waɗannan dalilai, kuwa su ne kamar rowa:

Jagora: *Ni dai na rena tasu 'yan taurin zamani na na Ummaru*
*: Ba son su ba mu komi sai tsigwami,*
*: Sai son muy masutaki banza su sha.*
(waƙar Mani Jiko)

Bisa al'adu ɗan taru ko ɗan farauta ko kuma ɓarawo ya sadu da makaɗinsa yakan yi masa alheri gwargwadon karfinsa. Ko ya yi masa waƙa kuwako bai yi masa ba idan ya rigaya ya yi masawaƙa, to, da dalili, idan ma bai yi masa ba wannan zai iya zama kamar toshi yadda zai ji daɗi ya yi masa waƙar. Amma a nan sai ga wasu waɗanda aka yi wa waƙar ba su ba da komi ba. Shi ne Kassu yake yi wa ire-irensu habaici da cewa ba su yin kyauta, burinsu shi ne a yi 'masu taki banza su sha.

Bayan haka Kassu Zurmi yana amfani da wani irin nau'i na habaici watoi maimakon ya sakaya sunan mutum ya faɗi wasu kamanni nasa, sai ya yi duka, wato ya faɗi, suna kuma ya bayyana kamanni irin wannan habaici shi aka kira habaici ƙiri-ƙiri:

Jagora: *Dole gudu, dole ba ka baya Gondau na Garba*
*: Hwaɗa ma Aikan im ba ya ba ka baya sai ka kasai,*
*: Yanzu gaban wani ya hwaɗi wanda yas so ƙarya damu.*
(Waƙar Gandau)

Da mutum ya saurari wannan, ko kuma ya karanta, zai fahimci ko da wa ake, domin kuwa ga sunan wanda aka yi wa habaici nan Aikau:

Jagora: *Mai doro ba ya shan bugu Na-magaji,*
*: Anne wadda kab bugai sai bwaɗuwa*
*: Kaico ashe ɗan kamag ga shuru ƙaryab banza garai.*
(Waƙar Gandau)

A nan ma Kassu Zurmi ya bayyana kamannin wanda ya ke yi wa habaici ga waɗanda ba su san sunansa ba. Haka kuma bayan ya faɗi ga waɗanda suka san shi, sai ya bayyana kamanninsa domin ƙarin bayani.

Kafin ƙarasa wannan bayani, ana ganin akwai muhimmanci a duba wani nau'i na habaici shi ne, maimakon a yi wa mutum ɗaya sai a yi wa gari ko garuruwa.

A cikin waƙarsa ta Manin Jiko
Jagora: Barkeji ba maza sai mata na Garba,
: Gandau sauran waɗanda an nan mazanku ne,
: Gidan Goga yanzu ba maza sai mata na Garba,
: Gandau sauran waɗanda ac ciki bayanku ne.
: Rukudawa yanzu ba maza sia mata na Garba
: Gandau saurna waɗanda an nan kai ad dasu.
: Sun bi ka sun bi Allah daɗa kau na Garba.
(Waƙar Gandau)

Wannan habaici an yi shi ne ga garuruwa uku, amma a ƙashin gaskiya ana yi ne ga "mazajen" da suke cikin waɗannan garuruwa. Abin da Kassu yake son ya faɗi shi ne dukkan 'yan farauta na cikin waɗannan garuruwa ragwaye ne domin kuwa mutum ɗaya, gwarzonsa, ya gagare su.

Wato kenan habaici ya ƙunshi yi da mutum da magana a ɓoye Kassu yana amfani da nau'oin habaici. Yana yin habaici dangane da gazawar mugum a fagen yaƙi. Yana kuma yi saboda rashin yi masa kyauta. Haka kuma yana yin habaici ƙiri-ƙiri.daga ƙarshe kuma akwai habaici wanda yake yi wa jama'a da dama maimakon mutum ɗaya.

## 1.6 Sakamakon Bincike

Bayan wannan maƙalar ta zo ƙarshe, akwai waɗansu abubuwa da maƙalar ta gano a matsayin sakamakon bincike. Kaɗan daga cikinsu sun haɗa da;

- An gano cewa yana amfani da habaice-habaice a cikin waƙoƙinsa
- Wasa kai-tsaye waɗansu kuma a kaikaice
- Sai dai kuma ya san da waɗanda yake yi wa habaicinsa

## 1.6 Kammalawa

Daga abin da ya gabata, a cikin wannan muƙala akwai tabbacin cewa wasu waƙoƙin Kasssu Zurmi na ɗauke da habaici. Musamman makaɗin ya jejjefa habaici a cikin zubin ɗiyan waƙoƙin. Har wa yau muƙalar ta ƙawata bayani ta hanyar kawo tarihin Alhaji Kassu Zurmi da nau'o'in waƙarsa da wasu habaitai a cikin waƙar ɓarayi, farauta, tauri, tare da kawo misalai da sharhi daga zubin ɗiyan waƙoƙin da aka duba.

**Manazarta**

Ado, A. (2017:84). *Ra'o'in Bincike kan Rayuwar Hausawa*. Katsina Kanki Classical Media Enterprises.

Dangambo, A. ( 2007) *Danrayar Gadon Feɗe Waƙa*, Zaria Amana Publishers.

Gada M.M da Hadiza S.S. ( 2020) Shagari Journal of Languages, Shehu Shagari College of Educatiion, Sokoto

Gusau, S. M. (2005). *Makaɗa da mawaƙan Hausa.* Kano;Benchmark Publishers Ltd

Gusau, S. M. (2009). *Diwanin waƙoƙin Baka: Zaɓaɓɓun matanoni na waƙoƙin Baka na Hausa*. Kano Century Research and Publishing Ltd

Gusau, S.M ( 2003), *Jagoran Nazarin Waƙar Baka.* Kano: Benchmark Publishers, Shafi naXIII

Kamusun Hausa: ( 2006) Jami'ar Bayero. Cibiyar Nazarin Harsunan Najeriya.

Magaji A. (2016) *Kassu Zurmi da Waƙoƙinsa*. Published by Spectrum Books Limited Ibadan, Nigeria.

Umar, M.B (1980). *Adabin Baka Don Makarantun*. Zariya: Hausa Publications Center, Shafi na 13.

Yahya A.B (1997). *Jigon Nazarin Waƙa*. Kaduna: FISBAS Media Services, Shafi na 4.

Yahya A.B (2012).Waƙa: Ma'ana da Dabi'a da Ginshiƙanta. A cikin *Champion of Hausa Cikin Hausa A Festschrift in Honour of DalhatuMuhammad*. Department of African Languages And Cultures, Faculty of Arts, Ahmadu Bello University, Zaria.